Jerin Littafan Shi'a Na 7

# Zuwan

# Shi'a

# Nijeria

Umar Labɗo

بِسْمِ اللهِ الرَّحْمَنِ الرَّحِيمِ

Asalin yaɗuwar Shi'a a Nijeria ya fara a tsakanin matasa, yawanci 'yan makaranta, masu aikin yaɗa addinin Musulunci waɗanda aka san su da sunan 'Yan Uwa Musulmi. Wannan suna fassara ce kai tsaye ta sunan wata Ƙungiya, *Al'ikhwanul Muslimun,* wacce Imam Hassan Albanna ya kafa a ƙasar Masar a cikin shekarun 1930. Babbar manufar ƙungiyar shi ne mayar da Musulmi zuwa ga hukunce – hukuncen Musulunci a kafatanin fagagen rayuwarsu wanda ya haɗa da fagen siyasa, tattalin arziƙi, tarbiya da zamantakewa da kuma dangantakarsu da waɗanda ba Musulmi ba. Kungiyar ta yaɗu a yawancin ƙasashen Musulmi ciki har da Nijeriya.

Tare da ƙungiyar 'Yan Uwa Musulmi akwai ƙungiyar Ɗalibai Musulmi ta Nijeriya, watau M.S.S. wacce aka kafa ta shekaru 50 da suka wuce. Waɗan nan ƙungiyoyi biyu sashen su ya haɗe da sashe kuma suna yin nashaɗinsu a jami'o'i da manyan makarantun ƙasar nan. A wani yayi nashaɗinsu yana shafar 'yan makarantun sakandare ta hanyar tarukan horaswa da suke shiryawa ɗaliban ƙananan makarantu a lokacin hutu. Masu shagala da aikin da'awa a ƙarƙashin inuwar waɗan nan ƙungiyoyi yawancinsu matasa ne maza da mata masu karatun fannonin ilmi dabam – daban, kamar Kimiya da Likitanci da Tattalin Arziki, amma kaɗan ne daga cikinsu suke karanta Musuluncin kansa. Wannan ya sa, koda yake suna da son Musulunci ga kuma gafin ƙuruciya, amma suna da ƙarancin ilmin addini. Saboda haka a lokacin da Shi'a ta shigo ƙasar nan, a kan doron juyin juya hali na Musulunci (!) na ƙasar Iran da kirarinsa mai ɗaukar hankali na kafa jumhuriyar Islama da zartar da hukunci da Shari'a, sai yawancin waɗannan samari

suka hau jirgin Shi'a da tikitin juyin Islama. Daga cikin waɗan nan samari akwai Malam Ibrahim Ya'aƙub Alzakzaki.

**Alzakzaki da Yaɗuwar Shi'a**

Sunan Zakzaki ya fara fitowa a farkon shekarun 1980 lokacin da, bayan kammala karatunsa a fannin Tattalin Arziƙi daga Jami'ar Ahmadu Bello ta Zaria, ya ƙi ya je aikin bautar ƙasa, watau N.Y.S.C. saboda, kamar yadda ya ce, shi ba ya bautawa ƙasa; Allah kaɗai yake bautawa. Duk da raunin wannan magana da rashin fahimtar addini da take nunawa a fili, wannan mataki da Zakzaki ya ɗauka ya ba shi farin jini kuma ya mayar da shi tamkar wani gwarzo a idanun matasa waɗanda wutar son addini take ci a zukatansu amma ƙwaƙwalensu sun yi duhu duɗum saboda jahilci. Zakzaki ya wayi gari ana lasafta shi daga cikin shugabannin ɗalibai da matasa masu sha'awar addini.

Ba'a daɗe da haka ba, sai mahukuntan ƙasar Iran masu bin tafarkin Shi'anci, a cikin ƙoƙarinsu na neman goyon bayan Musulmin duniya musamman a kan yaƙinsu na shekaru takwas da ƙasar Iraƙi, suka riƙa gayyatar malamai da matasa masu sha'awar addini daga ko wane ɓangare na duniyar Musulmi domin su halarci bikin shekara – shekara da suke yi don tunawa da nasarar juyin juya halinsu. Zakzaki na daga cikin waɗanda aka gayyata daga Nijeriya.

Mahukuntan Iran waɗanda suke ɗaukar nauyin baƙinsu zuwa da komowa, suna nunawa baƙin karamci, suna girmama su ainun kuma ga alama suna ba su ɗan goro a matsayin sallama. Banda wannan, suna ƙoƙarin cusa wa baƙin nasu aƙidar Shi'anci ta hanyar laccoci, muhalarori, tarukan ƙarawa juna sani da kuma kyautar littafai masu yawa. Ga alama ta wannan hanya sun yi nasarar ribace wasu da shigar da su tafarkinsu kamar Zakzaki, wasu kuwa sun gane makircinsu sai suka

raba gari da su.  Daga cikin waɗanda aka gayyata daga Nijeriya kuma amma ba'a yi nasarar janye su zuwa Shi'anci ba akwai Malam Abubakar Tureta daga Kaduna da Malam Abubakar Jibril daga Sakkwato wanda ya zama a sahun gaba wajen yaƙar Shi'anci a Nijeriya.

Alaƙar Zakzaki da Iran ta ci gaba da yin ƙarfi a hannu guda, a ɗaya hannun kuma shahararsa ta bunƙasa, kuma magoya bayansa suka ƙara yawa, a yayin da ya buɗe ressa a yawancin jihohin arewacin ƙasar nan, yana kira da sunan gwagwarmayar kafa hukuncin Musulunci da yaƙar waɗanda ya kira ɗagutai.

Mabiyan Zakzaki sun yi ban gaskiya da shi ainun, sun yarda da shugabancinsa har suna ganin wanda duk bai ɗauke shi a matsayin shugaba ba kamar shi ba Musulmi ba ne, suna cewa wanda ya mutu bai yi masa mubaya'a ba to ya mutu mutuwar Jahiliya.  Shi kuwa ya yi amfani da amince masa da suka yi, ya riƙa gabatar musu da koyarwar Shi'a da aƙidojinsu sannu a hankali kuma koda yaushe aka tsorata su da kusancin shugabansu da Iran, sai ya ba su tabbacin cewa shi babu abinda ya haɗa shi da Iran sai gwagwarmaya da yaƙar Amurkawa da Yahudawa da ɗagutai.  Amma kuma a hannu guda, Zakzaki ya ci gaba da shigo da alamu da bukukuwan Rafilawa kamar babbaƙun rawuna, bikin Ashura, da sauransu.

Haka nan gogan naka ya ci gaba da *taƙiya,* yana yaudarar almajiransa da magoya bayansa har ranar da dubunsa ta cika.  Wata mujalla daga cikin irin mujallun da ake bugawa a ƙasar Iran ana aikowa da su Nijeriya ta buga wata maƙala wacce a cikinta aka ci  zarafin Sahabin Annabi (SAW) mai shuhura watau Abu Huraira (R.A).  Wannan ya tayar da hankalin wasu daga cikin mabiyan Zakzaki inda suka nemi ya fito fili ya la'anci wannan maƙala amma ya ƙiya. Wannan shi ya buɗe idanun da yawa daga cikin mabiyansa, waɗanda a da jahilci

da bin son zuciya ya rufe idanun nasu. Daga nan aka samu wani reshe a cikin mabiyan Zakzaki wanda ya yi ta matsawa malamin lamba a kan ya fito fili ya bayyana matsayinsa dangane da ko Shi'a yake yi ko a'a. Zakzaki ya ci gaba da noƙewa har dai daga bisani tusa ta ƙurewa bodari kuma gaskiya ta yi halinta. A cikin shekarar 1995 aka yi uwar watsi bayan wani taron ƙure ƙarya da aka yi wa Zakzaki a hedkwatarsa a Zaria. Mabiyansa da yawa, ciki har da manyan almajiransa, suka ɓalle, suka yi shelar barrantarsu da Zakzaki da tafarkinsa na Rafilanci kuma suka kafa tasu ƙungiya ta yunƙurin jaddada Musulunci a kan tafarkin Ahlus Sunna, Jama'atu Tajdidil Islam (J.T.I.), a ƙarƙashin shugabancin Malam Abubakar Mujahid. A yanzu asirin Zakzaki ya tonu kuma *taƙiya* ta ƙare, amma kash! Biri ya riga ya yi ɓarna.

**Dalilan Yaɗuwar Shi'a a Nijeriya**

Akwai dalilai masu yawa da suka taimaka wajen yaɗuwar tafarkin Rafilanci a nan ƙasar. Za mu duba muhimmai daga cikinsu.

**Dalili Na Farko: Gazawar Malamai**

Dalili na ɗaya kuma mafi muhimmanci, shi ne gazawar malamai a shugabancin jama'a da shiryar da su, da yi musu jagora da katangance su daga ɓata. Domin famintar wannan dalili za mu kasa malamai gida uku.

1. Malaman zaure, ko kuma malaman buzu kamar yadda ake kiran su a wasu wurare. Wannan kashi a cikin malamai su ne mafi girma, mafi alƙadari kuma mafi ƙima a idanun mutane. Amma duk da girma da ƙimarsu da muke gani, za mu rufe ido mu faɗi gaskiya game da su domin gaskiya ta fi ko wane mai ƙima ƙima.

Matsala ta farko da malaman zaure, yawancin su, shi ne imma dai suna da ƙarancin sani ko kuma ilminsu ya saɓa Sunna. Ɗauki ilmin Tauhidi ga misali,

wanda shi ne mafi muhimmanci kuma mafi ɗaukakar dukkan ilman Musulunci. Har yanzu malamanmu na buzu ba su rungumi tafarkin Sunna ba a babin Tauhidi; Tauhidinsu imma Ash'ariya ne ko kuma Tauhidin masu Ilmul Kalam wanda yake da tushensa a wajen Mu'utazilawa ko Falasifawa.

A fannin Fiƙihu, wanda shi ne fannin da malaman zaure suka yi fice, yawancinsu a Fiƙihun Malikiya kawai suka tsaya. Idan mutum ya duba cewa banda sauran mazhabobi uku fitattu, watau Hanafiya, Shafi'iya da Hanbaliya, akwai mazhabobin Zahiriya da Zaidiya, banda mazhabobin ɗaiɗekun malamai waɗanda ba su samu yaɗuwa ba kamar mazhabar Imam Thauri da Imam Auza'i da sauransu, sai mutum ya ga cewa babu shakka malamanmu kaɗan suka ɗebo a Fiƙihun Musulunci. Ba'a maganar fannin *Usulul Fiƙhi.* Kuma ko a Malikiya ma, wasu littafai ne ƙididdigaggu suke laƙema, wasu manyan littafan mazhabar yawancinsu ba su karanta su, kamar *Tafsirin Kurɗubi* da *Tafsirin* Abubakar Ibnul Arabi, da *Altamhid* na Ibnu Abdilbarri da *Bidayatul Mujtahid* na Ibnu Rushd, da sauransu. A nan ba kuɗin goro muke yi wa malaman ba; amma muna bayyana halin yawancinsu ne.

A fannin Tafsiri kuwa, ya ishe ka manuniya cewa a ƙasar Hausa duka idan mutum ya ce, "Na tafi wajen jalalaini," to wajen karatun tafsiri yake nufi saboda tafsiri shi ne jalalaini kuma jalalaini shi ni tafsiri. Wannan yana nuna yadda malamanmu suka tsaya a kan littafin *Tafsirul Jalalaini* na Jalaluddinil Mahalli da Jalaluddinis Suyuɗi kawai a koyo da koyarwarsu na fannin Tafsiri. Idan aka duba cewa wannan littafi bai kai matsayin moɗa guda ba a cikin kogi dangane da abinda aka rubuta a fannin Tafsiri, sai a ga cewa tabbas abinda malamanmu suka rasa ya fi abinda suka samu a cikin wannan fanni. Bari batun ilmin *Usulul Tafsir.* A nan ma, ba kuɗin goro muke yi wa malaman ba; amma hukunci a kan mafi yawa ake yin sa, mafi ƙaranci togewa ne.

Matsalar Luga a wajen malaman buzu makomarta ita ce ga matsalar manhaja da tsarin koyarwa. Koyon Luga yana da rukunai uku: karatu da rubutu da furuci. Ga alama malaman zaure karatu kaɗai suke yi saboda a tsarin karatun zaure babu zancen a bayar da aiki a rubuto, watau abinda ake cewa da Larabci "tamrinat" ko "tamarin", ko kuma da Turanci "exercises". Wannan ya sa koda yake malaman zaure yawanci suna da babbar taska ta ɗaiɗekun kalmoni, "vocabulary", amma magana da Larabci tana yi musu wuya, haka nan rubutawa. Kuma koda yake ana iya lura cewa malaman buzu gwanayen rubutun waƙa ne da Larabci, makomar wannan, wata ƙila, shi ne cewa ita waƙa 'yar kyaikwayo ce.

Haka nan a fannonin *Hadisi* da *Tarihi* da *Sira* da *Firaƙ*; malaman buzu, in ka ɗauke su gaba ɗaya, suna da ƙarancin rabo a cikin waɗan nan ilmai. Rashin ilmin *Firaƙ*, watau ilmin ƙungiyoyin bidi'a da aƙidojinsu, shi ya sa malaman zaure suka rasa ta yi a gaban kogin Shi'anci yayin da ya yi ambaliya domin ya tafi da matasan Musulmi. Manyan littafan da aka rubuta a ilmin *Firaƙ* kamar A*lmilal wal Nihal* na Shahrastani da *Maƙalatul Islamiyina wa Ikhtilaful Musallina* na Imam Abul Hassan Al'ash'ari da *Alfarƙu bainal Firaƙ* na Shaihul Islami Abdulƙahir Albagdadi da *Alfisal fil Milal wal Ahwa'i wal Nihal* na Ibnu Hazm Al'andalusi da sauransu, yawancinsu ko sunayensu ba su taɓa ji ba.

Wannan ya sa suka ɗauka cewa wai Shi'anci wani wasan yara ne wanda za su bari in sun girma! Idan aka ce su bincika abinda yake faruwa a tsakanin Rafilawa sai su ce, haba wannan hayaniyar ƙuruciya ce suke yi, za su bari ne. Sai ga shi waɗan nan malamai waɗanda suka tashi zaune tsaye a saboda wasu 'yan ƙungiyoyi da suka ce wai suna zagin waliyai, sai ga shi ana zagin Sahabban Annabi (SAW), ana kafirta su, amma sun yi shuru. Saboda haka malaman suka kyautata alwala amma suka gaza sallah!

Abinda ya gabata dangane da ilminsu ne; amma idan muka duba ayyukansu sai mu ga abin mamakin. Mun gabatar da bayani cewa a cikin malaman Musulunci a nan ƙasar, malaman zaure su ne mafi yawa, mafi alƙadari kuma mafi ƙima a idanun mutane. Abinda ya sa suka zama haka shi ne cewa su magadan Jihadin Shaihu Danfodiyo ne. Amma a yau, ayyukansu da halayensu sun saɓa da na malaman Jihadi. Malaman Jihadi sun yi ilmi mai zurfi, kuma littafan da suka bari suna shaidawa da haka, amma malamanmu na yau abin ba haka yake ba. Shaihu Usmanu ya rubuta kimanin littafai 90, Shaihu Abdullahi kimanin 70; Muhammad Bello ɗan Shaihu kimanin 80; Nana Asma'u kimanin 55; amma malamanmu na yau, saboda gafala rubutun ma laifi suka ɗauke shi. Idan ka ce su rubuta littafi sai su ce wai ba su gama da waɗanda aka riga aka rubuta ba; idan kuma kai ka rubuta sai su ce ka yi karambani. Alhali Shaihu Usmanu, a cikin littafinsa *Najmul Ikhwani,* yana kira ga Musulmi da su riƙa karanta littafan malaman zamaninsu, saboda malaman ko wane zamani su suka fi sanin matsalolin wannan zamanin, kuma wajibinsu ne su nemawa matsalolin magani.

Malaman jihadi sun yi wa'azi, malaman buzu ba sa yin wa'azi sai kaɗan. Malaman jihadi sun yaƙi bidi'a, malaman zaure su bidi'ar suke yaɗawa kuma duk wanda yake yaƙi da bidi'a to su shi ne abokin gabarsu. Malaman jihadi sun nesanci sarakai da masu mulki, na yanzu kuwa shige musu suke yi. Malaman jihadi sun yi jihadi kuma sun jaddada addini, malamanmu na yau ba su san ko inda za'a kama bakin zaren ba. Malaman Jihadi sun tsaya tsaiwar daka, sun yi gwagwarmayar tabbatar da gaskiya da tsai da adalci, malamanmu na yau cewa suke yi yanzu zamanin yin shiru ne da lazimtar cikin gida, kamar yadda wani babban malamin zaure ya faɗa wa Shaihu Abubakar Mahmud Gumi.[1] Malaman jihadi sun gina al'umma, malaman buzu sai aikin gina gidajensu na gado. Ko

[1] Duba **Where I Stand** na Abubakar Mahmud Gumi, bugun Spectrum Books, Ibadan-Nijeriya, 1992, shafi na 51.

wane malami ya ƙasaita sai ka ji ya naɗa khalifa, wai ɗan da zai gaje shi. Ko waye ya ce musu ilmi gado ne? Malaman jihadi sun ce a yi sana'a (duba *Ahkamul Makasib* na Muhammad Bello) su kuwa yawanci ba sa sana'ar, balle su ce wani ya yi, sai cin abinda suke kira albarkacin makaranta!! Wani malamin ma har faɗa yake yi don me za'a ce Musulmi su daina bara!! Kuma ƙarya yake yi; shi 'ya'yansa ba sa bara.

Kai a yau ta kai cewa malaman buzu da yawansu, ba wai kawai sun raba gari da tafarkin Shaihu Ɗanfodiyo ba da da tarihinsa da koyarwarsa, a'a yaƙar sa ma suke yi! Sun ƙaurace wa littafansa da ilminsa da koyarwarsa. Mutum zai yi shekara guda cur bai ji sunan Ɗanfodiyo ya gudana a bakin ɗayansu ba a wajen karatu ko wa'azi. Maimakon haka, sun rungumi koyarwar wasu jahilan malamai waɗanda bas u zo ƙasar nan da kome ba sai diwanin waƙe-waƙe.

Wannan shi ne halin yawancin malaman azure, kuma shi ne tushen kusan dukkanin matsalolin da muke fama da su a yau. Don haka babu mamaki idan ba su taka rawa ta ku-zo- ku-gani ba wajen hana yaɗuwar Shi'anci a ƙasar nan.

2. Kashi na biyu na malaman shi ne wanda za mu kira da sunan Ustazai. Wannan kashi ya haɗa da dukkan waɗanda suka yi karatun addini amma a zamanance, kamar waɗanda suka halarci makarantun Haya Muslim kuma suka yi karatun diflomomi ko digiri na fannin nazarin addinin Musulunci ko Shari'a a manyan makarantu da jami'o'in ƙasar nan. Kuma ya haɗa da waɗanda suka yi karatu a jami'o'in ƙasashen Larabawa da sauran ƙasashen Musulmi. Waɗan nan yawanci suna da kyakkyawar manhaja ta koyon karatu kuma ilminsu yana da faɗi da zurfi koda yake wasunsu, kamar waɗanda suka fita daga jami'o'in ƙasarnan, ilmin nasu faɗi gareshi kawai amma ba zurfi. Sai dai duk da haka suna samun kyakkyawan harsashi wanda yake ba da dama ga duk wanda yake so cikinsu da ya

zurfafa. Suna tsakuro wani abu kusan daga ko wane fanni muhimmi na addinin Musulunci kamar Alƙur'ani da Hadisi (waɗan nan ba su da ƙarfi a manhajojin jami'o'in Nijeriya); Fiƙihu da Usulul Fiƙihi, Falsafa da Tauhidi (a makarantun Nijeriya yawanci Tauhidin Ash'ariya ake koyarwa); Tarihi da Sira; da kuma fannonin Luga dabam – daban irin su Adab, Nahawu, Sarfu, Balaga da ressanta uku, Aruli, da sauransu. Samun ƙaƙƙarfan harsashe na Luga yana zama tamkar wani mabuɗi ga Ustazai wanda suke buɗe taskokin ilmi da shi.

Kamar yadda Ustazai suka sha bamban a wajen ilminsu, da mai zurfin ilmi da mai cikin cokali, haka nan suka sha bamban wajen ayyukansu da halayensu da sadaukar da kansu ga addini. Akwai masu aƙidar Salaf, masu bin Sunna da yaƙar bidi'a, kamar yadda akwai 'yan gargajiya wajen aƙidarsu da fahimtarsu da rungumar bidi'a. Daga cikin waɗan nan na biyun akwai waɗanda suka fito daga gidajen malaman zaure, waɗanda suka fito daga gidajen sarautar gargajiya da masu karkata ga ɗariƙun Sufaye. A cikin Ustazai akwai masu yin wa'azi da waɗanda ba sa yi, da masu yaƙar bidi'a da 'yan ba-ruwanmu da waɗanda suka sadaukar da kawunansu domin koyar da mutane da aikin da'awa da waɗanda ba sa koyarwa sai dai a aji inda ake biyan albashi.

Yawanci waɗanda suka wayar da kan Musulmi dangane da tafarkin Rafilanci, suka bayyana ɓacinsa da sharrinsa da ɓatansa, suka yi fama don dakatar da yaɗuwar Shi'anci a tsakanin Musulmi daga cikin wannan kashi suke. Daga cikinsu akwai waɗanda suka yi amfani da koyarwa da wa'azi wajen yaƙar Shi'a kamar Shaihu Abubakar Mahmud Gumi, wasu sun yi amfani da huɗuba kamar Shaihu Abubakar Jibril Sakkwato, wasu sun yi amfani da alƙalumansu kamar Shaihu Aminuddini Abubakar Kano wanda ya fassara littafin *Alkhuɗuɗul Arida* na Muhibbud Dini Alkhaɗib zuwa harshen Hausa wanda a karon farko ya fallasa asirin Shi'a ga jamhurun Musulmi waɗanda ba sa karatun Larabci ko Turanci.

3 Saboda rashin kalmar da ta fi, za mu kira kashi na uku na malaman da sunan Burazozi wanda wannan hausancewa ne na kalmar “brothers” ta Turanci wace take nufin ‘yan uwa. Abinda nake nufi da burazozi, ko kuma ‘Yan Buraza kamar yadda aka fi sanin su, su ne mutane, yawanci matasa, waɗanda suke da son Musulunci a zuci amma kuma galibi suke da ƙarancin saninsa. Yawanci suna sanin Musulunci ta hanyar sauraron laccoci a wurin taruka, karanta ƙasidu da maƙalu a cikin jaridu na yau da kullum da kuma mujallu masu kulawa da al’amuran Musulmi. Yawancinsu ɗalibai ne masu karatun fannoni dabam-daban a manyan makarantu da jami’o’i kamar fannonin kimiya, fasaha, tattalin arziki, likita, lauya da sauransu. Kaɗan ne daga cikinsu suka karanta Musulunci kuma a mataki na ƙasa ainun, imma I.R.K. a makarantun sakandare ko kuma ƙaramar faifa ta aro a jami’a.

Kamar yadda na faɗi a baya, yawancin waɗannan matasa ne masu tsananin son addini da kishin sa amma kuma babu wadatar ilminsa. Idan ka haɗa ƙarancin sani da tsananin kishi da gafin ƙuruciya, sai ka samu wani kwaɗo mai haɗari. Kuma da yake yawanci suna jin Turanci, harshen da shi ne ake yin amfani, kuma ake burga, da shi a makarantu, wannan sai ya ba su damar shaƙe wuyan makirfon da faɗi a saurare su, koda abinda za su faɗi ɗin ba shi da nauyi ainun. Wani babban abinda yake ƙara tauye su shi ne rashin jin Larabci kuma kamar yadda aka sani duk wanda bai jin Larabci to ba ya shan kunun Musulunci sai dai ya sha farau – farau. Wannan kashi na “malamai” daga cikinsu ne yawancin ‘yan Shi’a suka fito, ciki har da madugunsu Malam Zakzaki.

Wannan bayani duka ba yana nufin cewa wannan kashi na malamai bai yi wa Musulunci kome ba; a’a. A haƙiƙa ‘Yan Buraza sun toshe wata babbar kafa a makarantunmu wacce, musamman a shekarun 1970 da 1980, ba mai iya toshe ta sai su. Sun taimaka ainun wajen tsayar da ibadoji, kamar sallah da azumi, a makarantu, sun tari ƙalubalen ƙungiyoyin Kirista kuma sun taimaka wajen

yaƙar malamai da ɗalibai masu karkata ga tafarkin Gurguzu a jami'o'inmu a lokacin da Kwaminisanci yake yaƙar addinai da al'adu a ƙasashe masu tasowa.

Sai dai wannan kashi na malamai, da yawa daga cikinsu, bayan sun manyanta kuma sun taka matakin shugabanci da tasiri a cikin al'umma, har yau abin takaici suna nan suna yaɗa Shi'a, wasu a kan rashin sani wasu kuma a bisa ganganci. Daga cikinsu, ga misali, akwai wani ɗan jarida mai ƙima a idanun makaranta, wanda ya yi rubutu a wata jarida wacce ake mata kallon ta Musulmi ce, yana cewa wai ƙiyayyar da Larabawa suke nuna wa mutanen Iran ƙiyayya ce da aka gina ta a kan ƙabilanci, yana nufin saboda su 'yan Iran Farisawa ne ba Larabawa ba, kuma wai saɓanin dake tskaninsu ba na aƙida ba ne. Babu shakka wannan ɗan jaridar imma dai ya shiga fagen da ba shi da sani a kai, abinda bai dace da ɗan jarida mai mutunci da amana ba, ko kuma yana yaudarar makarantansa ne da gangan.[1]

Akwai wani Farfesan Tarihi (amma ba Tarihin Musulunci ba) wanda ya ba da lacca a munasabar bikin Ashura na 'yan Shi'a na shekarar 1432/2011 a Kano, inda ya ce wai ranar da Hussaini(RA) ya yi shahada ita ce rana mafi muhimmanci a tarihin Musulunci.

Abin mamaki! Ba ranar da Annabi(SAW) ya yi hijira zuwa Madina ba (wacce Sahabbai suka zaɓe ta, don muhimmancinta, ta zama rana ta farko a kalandar Musulunci); ba ranar yaƙin Badar ba (wacce Allah ya kira ta a cikin Alƙur'ani: **Yaumal Furƙani:** Ranar rabewa tsakanin ƙarya da gaskiya); ba ranar Sulhun Hudaibiyya ba (sulhun da Allah ya kira shi a cikin Alƙur'ani: **Fatahan Mubina**: Buɗi mabayyani); ba ranar Fatahu Makkata ba (ranar da aka kawo ƙarshen bautar gumaka a ƙasar Larabawa); a'a, ranar da Hussaini ya yi shahada ita ce mafi muhimmanci a tarihin Musulunci! Ban sani ba wannan jahilci ne daga ɓangaren Farfesan ko kuwa ya sha farfesun Iran ne, shi ya sa yake faɗin haka da gan-gan don ya ɓatar da mutane?

---

[1] Domin tabbatar da haka, duba littafinmu **Matsayin Musulmi a wajen 'Yan shi'a.**

Kuma wasu jaridu da ake wa kallon cewa su na Musulmi ne sun ɗauko wannan bankaura ta Farfesan, sun buga ta, suna yaɗa ta a tsakanin al'umma. Shin rashin sani ne wannan ko kuwa wata ƙullalliya ce? Ta yaya 'yan jaridarmu za su jahilci addininmu? Ko ta ƙaƙa mutanen da aikinsu ne ilmantar da jama'a da faɗakar da su da wayar da su, za su komo suna yi musu rufa-ido?

Na karanta wata maƙala a cikin jaridar **Daily Trust** fitowar Alhamis, 23 ga watan Fabrairu, 2012 shafi na 52, inda wata ma'aikaciyar jaridar mai suna Hajiya Wance ta ruwaito wani malamin Shi'a yana zargin Sayyidina Abubakar da Sayyidina Umar, Allah ya ƙara musu yarda, da cewa wai sun yi mubaya'a ga Ali binu Abi Ɗalib(RA) a kan khilafa a gaban Annabi(SAW) amma bayan rasuwar Annabi ɗin sai suka warware wannan mubaya'ar.

Sai na yi mamaki yadda jaridar za ta tallata wannan zargi na Shi'a tare da cewa zargin ya saɓa da tarihi ingantacce, kuma tare da cewa zargin yana tattare da ɓatanci ga waɗannan manyan Sahabbai. Na ce a raina da wani ɗan Majalisar Dattijai ne ko Majalisar Wakilai aka yi wa wannan zargi da wata ƙila jaridar sai ta tuntuɓe shi, ko ta tuntuɓi wani mataimakinsa, kafin ta buga zargin don ya kare kansa ko ya ƙaryata, kamar yadda jaridu masu mutunci suke yi. (Wani da ba na tuhuma da ƙarya ya tabbatar mun da cewa sun aike da martani daga baya, amma jaridar ba ta buga ba.)

Ita wannan musakar Hajiyar da ta rubuta maƙalar da Editanta jahili, ko munafuki, da ya buga ta ba su sani ba cewa warware mubaya'a babban laifi ne a Musulunci wanda bai kamata a dangana shi ga gama-garin Musulmi ba, balle Sahabi, balle shugabannin Sahabbai irin su Abubakar da Umar, musamman kuma da yake wannan mubaya'ar an yi ta da umarnin Annabi(SAW) kuma a gabansa. Dangana musu wannan laifi zargin su ne da aikata FASIKANCI.

Imam Muslim ya fitar da hadisi daga Abu Sa'id Alkhuduri(RA) ya ce: Manzon Allah(SAW) ya ce, "Idan aka yi mubaya'a ga khalifofi biyu to ku kashe na baya daga cikinsu."[1] Da yake sharhin hadisin, Imam Nawawi ya ce, "Ma'anar hadisin: Idan aka yi mubaya'a ga wani khalifa bayan an riga an yi ga wani, to mubaya'ar na farko ita ce ingantacciya kuma wajibi ne a cika ta. Sa'an nan

---

[1] **Sahih Muslim.**

mubaya'ar na biyun ɓatacciya ce kuma haramun ne a cika ta. Haka nan haram ne gare shi (khalifan na biyu) ya neme ta (mubaya'ar tasa)."[1]

Mai karatu yana iya gani a fili cewa waɗannan talukai biyu, ina nufin Hajiya musaka da jahilin Edita, sun taimaka wajen tallata wannan zargi na ƙarya kuma sun dangana wa Abubakar da Umar, Allah ya ƙara musu yarda, munanan abubuwa guda biyu: barin wajibi da aikata haram. Wannan da harshen Shari'a shi ake cewa fasiƙanci. Wata ƙila muna iya ƙarawa da wani abu na uku wanda ya fi biyun muni: saɓawa umarnin Annabi(SAW) da gangan, abinda yana iya zama kafirci, wanda kuma shi 'yan Shi'a suke nufi da wannan zargin tunda su a wajensu waɗannan Sahabban kafirai ne masu ridda. Wal iyazu billah!

Muna fata wannan zai zama gargaɗi ga masu karambani a cikin ilmin Musulunci da su sama wa kansu lafiya, su ƙyale masu ƙwarewa da fagensu.

## Dalili na Biyu: Jahilci

A yayin da malamai suka gaza sai jahilci ya samu filin baje koli. Juyin juya hali na ƙasar Iran ya faranta ran al'ummar Musulmi ganin yadda tutar Musulunci ta ɗaukaka da yadda daular kafirci mafi girma, Amurka, ta kunyata. Wannan ya sa Musulmi da yawa suka sha'afa da aƙidar mutanen Iran a lokacin da suka riƙa duban su a matsayin wani abin koyi da ya kamata kowa ya yi koyi da su. Da yawa daga Musulmi sun zaci cewa bajintar mutanen Iran da nasarar da suka samu ta 'yantar da kansu daga zaluncin Amurkawa da danniyar Turawan yammacin duniya baki ɗaya, sanadinta shi ne aƙidar Rafilanci da suka ƙudure. Wasu jahilai kuma suka riƙa zaton cewa munafunci da suke gani a wurin wasu sarakai da shugabannin ƙasashen Musulmi masu bin tafarkin Sunna tushensa shi ne aƙidarsu ta Sunna wace babu bore, ba gwagwarmaya, kuma babu ƙundumbala a cikinta. Wannan sai ya sa Musulmi da yawa, musamman matasa, masu tsananin son Musulunci da ƙin kafirci da jin takaicin halin

[1] Duba **Sharhu Sahih Muslim** na Imam Muhyiddin binu Sharaf Annawawi, bugun Darul Fikir, Bairut, 1401, mujalladi na 12 shafi na 231.

ƙasƙanci da koma baya da al'umma suke ciki, suka riƙa ganin sun sami mafita a cikin koyi da mutanen Iran.

Wani abu da ya ƙara wa mutanen Iran farin jini da haiba a idanun Musulumi waɗanda zukatansu suke cike da son Musulunci amma ƙwaƙwalensu wayam, shi ne wasu kalmomi masu ƙyalli da ƙyal-ƙyali da suka riƙa amfani da su kamar gwagwarmaya, barranta daga ɗagutai, gogayya da kafircin duniya, yaƙi da waɗanda suka kangarewa Allah Ta'ala, fatattaƙar Yahudawa da 'yanto masallacin Baitul Maƙdis, kafa jumhuriyar Islama, yin shahada wajen ɗaukaka addinin Allah, da irin waɗan nan kalmomin take da kirari waɗanda Rafilawa suka yi ta burgewa da su.

Ga alama irin waɗan nan kalmomi su suka burge Zakzaki da maƙarrabansa inda suka yi ta maimaita su kamar yadda akun kuturu take kyaikwayon abinda aka gaya mata ba tare da ta san ma'anarsa ba. Da waɗan nan kalmomi su ma suka ja gayya, inda komai na Iran ya zama abin yayi, kama daga babbaƙun rawunansu zuwa manyan alkebbunsu, kai har da sunayensu da laƙabansu, da tafiyarsu da maganarsu. Hotunansu da jaridunsu da mujallunsu da uwa uba littafansu suka cika ko ina. A cikin wannan ruɗu, mugunyar aƙidarsu ta yi saraf ta shige ƙwaƙwalen dake haihai. Da haka ne Shi'a ta yaɗu a Nijeriya a ƙarƙashin inuwar gazawar malamai da gafalarsu.

**Dalili na Uku: Talauci**

Talauci shu'umin abu ne. Yana zama haɗari ga lafiyar mutum da tunaninsa; ga halayensa da ɗabi'unsa; ga zamantakewar iyali da zaman lafiyar al'umma; kuma abinda ya fi kome haɗari, talauci yana iya mayar da Musulmi kafirai. Wannan ya sa Manzon Allah (SAW) a koda yaushe yake addu'a yana neman tsari daga talauci, kamar yadda aka ruwaito yana cewa, "Ya Ubangiji, ina neman tsarinka daga

talauci da ƙaranci da ƙasƙanci." (Abu Dawuda da Nasa'i). Kuma yana cewa, "Ya Ubangiji, ina neman tsarinka daga kafirci da talauci." (Abu Dawuda). Duba ka gani yadda ya gama tsakanin kafirci da talauci za ka fahimci cewa haɗarin talauci yana da girma.[1]

Talauci ya taka mugunyar rawa ta fuska biyu wajen yaɗuwar tafarkin Shi'anci a tsakanin matasa Musulmi a Nijeriya. Fuska ta ɗaya ita ce kasancewar matasa da iyayensu yawanci suna fama da talauci da rashin abin yi, don haka Rafilanci wanda yake cike da hayaniya da zanga-zanga da sauransu, sai ya zama wata mafita ce ga matasa da za su fita daga zaman banza da suke fama da shi kuma su sami abin yi wanda zai shagaltar da su daga matsalolin rayuwa waɗanda suka dabaibaye su. Fuska ta biyu ita ce kasancewar da'awar 'yan Shi'a da harakarsu ta ɗauki salon zuga talakawa a kan masu mulki da attajirai ta yadda koda yaushe suke maimaita magana a kan ɗagutai da azzalumai wanda ya sa talakawan Musulmi, waɗanda a haƙiƙa an zalunce su ɗin, suka rufawa 'yan Shi'a baya domin huce fushi da fatan rama gayya a ƙarƙashin daular Shi'awa wacce suke fatan kafawa.

Yana da wuya a yi bayani filla-filla yadda gwamnatin ƙasar Iran ta yi amfani da kuɗi wajen yaɗa tafarkin Rafilanci a Nijeriya, amma kowa ya san da walaki wai goro a miya. A lokacin da yake kan ganiyarsa, kafin Shi'ancinsa ya fito fili rabin mabiyansa su ɓalle masa, Malam Zakzaki tare da gwamnoninsa na jihohi, watau amir-amir da ya kafa a jihohi, duka suna rayuwa maya-maya, irin rayuwar attajirai masu hannu da shuni. Banda katafaren gidan da ya gina a garinsu Zaria, malamin kuma yana more kayan alatu kamar zunduma-zunduman motoci, kayan sadarwa na zamani, karikicen lantarki da sauransu. Wannan kuma shi ne halin manyan maƙarrabansa waɗanda suke a hedkwatarsa a Zaria da kuma waɗanda suke a

[1] Domin ganin hadarin talauci da muninsa, sai a duba **Mushkilatul Faqar wa Kaifa Alajahal Islam** na Yusuf Alqaradawi, bugun Maktabatu Wahaba, Alqahira, 1415/1995, shafi na 12-25.

jihohi. Saboda haka muke ganin cewa mutanen, kasancewar ba sa yin aikin gwamnati ko kamfani tunda wannan a ganinsu aikin ɗagutu ne, ba za su rasa samun ɗan hasafi ba daga wasu kafafe da ɓangarori wanda da shi ne suke tafiyar da harkokin ƙungiyarsu kuma su samu tsabar da suke watsa wa 'yan tsaki. Kuma idan muka dubi talaucin da mutanen ƙasar nan suke fama da shi, musamman Musulmi, tun daga farkon shekarun 1980, lallai tsaba na iya kai 'yan tsaki ko ina, in ya so ta baro su.

Sai dai a yanzu an samu canji a tunanin 'yan Shi'a da ayyukansu. Tuni suka daina ƙin aikin ɗagutu, tun da a yanzu ana samun su a cikin ayyukan gwamnati da na kamfani, bugu da ƙari a kan sana'o'I dabam-daban da suke yi. Hakan ya bas u dammar kafa tsari na tattara kuɗaɗe daga mabiyansu waɗanda suke amfani das u wajen jawo mutane da shigar da su tafarkinsu ta hanyar agaji da taimakon mabukata da sauransu.

**Dalili na Huɗu: Taɓarɓarewar Zamantakewa**

Wani dalili da ya taimaka wajen yaɗuwar Rafilanci shi ne taɓarɓarewar yanayin zamantakewa a tsakanin jama'a sakamakon sauye-sauye da suka faru a rayuwar al'ummarmu. Waɗan nan sauye-sauye sun haɗa da ƙaura daga rayuwar karkara zuwa rayuwar maraya, tasirin rayuwar wasu al'ummai a kanmu, raunin dangantaka tsakanin rukunan al'umma: tsakanin iyaye da 'ya'ya, manya da yara, shugabanni da talakawa, malamai da mabiya, da sauransu.

A yanzu kulawar iyaye ga yaransu ta yi ƙaranci ta yadda uba bai sanin inda ɗansa yake yin harkokinsa, ko da su wa yake hulɗa. Don haka bai san abinda ya koyo, ko ra'ayin da ya ɗauko ba. Ikon da manya ke da shi a kan yara a yanzu ya yi rauni. A da ana cewa yaro na kowa ne, kuma babban mutum ko dattijo yana iya tsawatawa yara koda bai san su ba kuma dole su saurare shi. Amma a yanzu ana

ganin yara suna cin karensu ba babbaka, babu mai ce musu ku ci kanku. A yau, talakawa sun daina mutunta shugabanni waɗanda suka rasa kwarjininsu saboda ƙarya da sata ('yan siyasa), jahilci da kwaɗayi (sarakan gargajiya). Mawadata sun rasa ban girman matalauta waɗanda suke ganin son abin duniyarsu ya yi yawa, kuma sun hana su haƙƙinsu na zakka. Malamai su ma girmansu ya faɗi a lokacin da mutane suka lura cewa suna gudu bayan abin duniya kuma sun miƙa wuya ga masu mulki da mawadata, sa'an nan sun bar matsayinsu na magadan annabawa.

Wannan sakwarkwacewa a cikin alaƙar rukunan al'umma junansu da juna ta bar matasa da gama-garin mutane a sake ba kariya, kuma wannan hali ya bai wa baraden Dujal, kamar shugabannin Shi'a, damar su baje kolinsu kuma su ci karensu ba babbaka. A sakamakon haka, magoya bayansu sai ƙara yawa suke yi koda yake abinda suke kira zuwa gare shi halaka ne da ɓata.

**Dalili na Biyar: Gazawar Masu Mulki**

Tsare Addini, *hifzud dini,* yana cikin manyan manufofin Shari'ar Musulunci, *Maƙasidul Shari'a,* kuma tabbatar da shi aikin hukuma ne. Daga cikin hanyoyin tsare addini akwai kiyaye shi daga dukkan abinda zai iya gurɓata shi, ko ya ɓata kyawunsa kamar bidi'o'i da camfe-camfe da tsurface-tsurface da duk wani abu da ya saɓa wa Alƙur'ani da Sunna.

Abin takaici ne cewa, tsarin siyasar da muke bi a yau tsari ne wanda babu ruwansa da addini. Saboda haka masu mulki suke ko-in-kula da abinda ya shafi addini sai fa idan ya zama zai amfani manufofinsu da maslahohinsu na siyasa. A sakamakon haka, Musulunci ya zama ba shi da gata, ko wane jahili, ko wani mugun malami Dujal sai ya shiga harkar addini ya yi abinda ya ga dama. Wani abin mamaki kuma shi ne, ko a jihohin da suke amfani da Shari'a a yanzu, abin bai canja ba. Koda yake an kafa ma'aikatun kula da harkokin addini a waɗan nan jihohi, amma ga alama waɗan nan ma'aikatu ba su ɗauki yaƙi da bidi'o'i a matsayin ɗaya daga cikin manyan ayyukansu ba. Wannan kuwa ba abinda yake

nunawa sai rashin fahimtar aikinsu, ko rashin sanin makamar aikin. Idan Ma'aikatar Kula da Harkokin Addinin Musulunci ba ta yaƙi bidi'a da masu yaɗa bidi'a ba, to mene ne amfaninta?

Ya kamata gwamnatocin jihohin Musulmi, kai har ma da gwamnatin tarayya, su fahimci haƙiƙanin Rafilanci da ɗabi'arsa. Yaɗuwar Shi'anci *MATSALA CE TA TSARO*, ba wai kurum matsala ce ta addini ko ta zamantakewa ba. Babu inda za'a samu Shi'a ta yaɗu a tsakanin Musulmi ba tare da sun kawo fitina da tashin hankali da zubar da jini ba. Wannan shi ne abinda tarihi yake shaida da shi kuma shi ne abinda muke gani a yau a dukkan ƙasashen da suke da 'yan Shi'a masu yawa kamar ƙasar Siriya da Pakistan da Iraƙi da Lebanon, da sauransu. Saboda haka zai zama tamkar wani kyakkyawan riga kafi ne idan Musulmin Nijeriya suka yiwa kansu ƙiyamallaili, suka tsayar da yaɗuwar Shi'a tun al'amarinta bai faskara ba. Kuma abin farin ciki shi ne, har yau ba'a makara ba; amma an yi kusa!

## Gudunmawar Sufaye ga Yaɗuwar Shi'a

Wani abu da zai iya shiga cikin dalilan yaɗuwar Shi'a a Nijeriya shi ne taimako da malamai da mabiyan ɗariƙun Sufaye suka bayar wajen hakan. Da ma dai akwai alaƙa mai ƙarfi a tsakanin Shi'a da Sufanci ta wajen kafuwarsu da aƙidojinsu. Malamai da yawa sun yi magana a kan wannan alaƙa, amma za mu ba da misali da maganar wani malami wanda babu mai zargin sa da cewa shi "mai tsananin ra'ayin Sunna ne," ko almajirin Ibnu Taimiyya ne, ko ɗan Wahhabiyya ne. Wannan malami shi ne Ibnu Khaldun. Ga abinda yake faɗi dangane da dangantakar Rafilawa da 'yan Ɗariƙa:

"Sa'an nan 'yan baya daga Sufaye suka fara magana a kan kashafi da al'amuran gaibu, kuma aƙidojin Hululu da Ɗayantakar Samuwa suka bayyana a

tsakaninsu.[1] Sai suka yi tarayya da Imamiyya (Shi'a 'yan dozin) da Rafilawa waɗanda suka ƙudure allantakar Imamai da Hululu. Kuma magana a kan Kuɗubi da Abdalu ta bayyana a tsakaninsu, kamar suna kwaikwayon aƙidar Rafilawa dangane da Imamai da Nuƙaba'u. Kuma suka aro aƙidojin Shi'awa."[2]

Har yau, Ibnu Khaldun yana faɗi a wani wurin dabam, "Sa'an nan waɗan nan Sufaye 'yan baya, masu maganar kashafi da al'amuran gaibu, suka zurfafa… Kuma magabatansu sun kasance suna gauraya da Isma'iliyya Rafilawa masu ƙuduri da Hululu da allantakar Imamai, tafarkin da ba'a san shi ba a wajen na farkonsu. Sai ko wanne (daga ƙungiyoyin biyu) ya ɗarsa daga tafarkin ɗan uwansa."[3]

To amma duk da wanan dangantaka da alaƙa mai ƙarfi a tushe da aƙidu, ƙungiyoyin biyu suna da bambance-bambance masu yawa. Ga wasu daga ciki:

Da farko, 'yan Shi'a suna kafirta Sahabban Annabi(SAW) baki ɗayansu in banda guda bakwai kawai, su kuwa 'yan ɗariƙa ba sa kafirta ko ɗaya daga cikin Sahabbai.

'Yan Shi'a suna zagin Sahabbai, suna yi musu ƙazafi, suna zagin Uwayen Muminai matan Manzon Allah(SAW) suna yi musu ƙazafi, su kuwa 'yan ɗariƙa ba sa zagin su, ba sa yi musu ƙazafi, maimakon haka suna girmama su, suna ƙaunar su.

'Yan Shi'a ba su yarda da khalifancin Khulafa'ur Rashiduna ba, Abubakar da Umar da Usmanu, sai Ali kawai, su kuwa 'yan ɗariƙa sun yi imani da khalifancin guda huɗun baki ɗaya.

---

[1] Dangane da ma'anar Hululu da Dayantakar Samuwa, sai a duba littafinmu **Sufanci da Aqidun Sufaye.**

[2] A duba **Muqaddimatu Ibni Khaldun** na Abdurrahman binu Khaldun, bugun Darul Kutubil Ilmiyya, Bairut, 1424/2003, shafi na 254.

[3] **Muqaddimatu Ibni Khaldun,** shafi na 386.

‘Yan Shi’a sun yi imani da khalifanci (ko imamancin) Imamai goma sha biyu: Ali, Hassan, Hussaini, Ali Zainul Abidin, Muhammad Baƙir, Ja’afar Sadiƙ, Musa Kazim, Ali Rida, Muhammad Taƙiy, Ali Naƙiy, Hassan Askari da na sha biyunsu Mahadi wanda suka ce wai an haife shi amma ya ɓuya yana ɗan shekara huɗu, kuma zai komo a ƙarshen zamani ya kafa daular Shi’awa. Su kuwa Sufaye, koda yake suna ƙaunar waɗan nan Imamai a matsayinsu na jikokin Manzon Allah(SAW), to amma ba sa ɗaukar su a matsayin khalifofi (tunda ba wanda aka taɓa naɗawa khalifa a cikinsu sai Ali kawai) kuma babu shakka ba sa ɗaukar su a matsayin Imamai da irin ma’anar da ‘yan Shi’a suke nufi da wannan kalmar.[1]

‘Yan Shi’a suna ƙuduri da cewa waɗan nan Imaman sun fi dukkan Annabawa da Manzanni da Mala’iku makusanta ga Ubangiji, su kuwa ‘yan ɗariƙa ba sa ban gaskiya da haka.

‘Yan Shi’a suna ƙuduri da cewa Imaman sun san gaibu, sun san abinda ya faru tun farkon halitta da abinda zai faru har bayan abada, kuma sun san abinda yake ƙunshe cikin zukatan bayi, su kuwa Sufaye ba sa ƙuduri da haka.

‘Yan Shi’a suna ƙuduri da cewa Alƙu’ani da yake hannun al’umma a yau, wanda kuma Musulmi ke tilawarsa a safe da yammaci, ba dai-dai yake ba, an yi ƙari da ragi a cikinsa, kuma wai Sahabbai ne suka yi wannan ƙari da ragin, su kuwa ‘yan ɗariƙa ba sa ban gaskiya da haka.

‘Yan Shi’a suna imani da cewa garin Karbala ta fi Makka da Madina falala, su kuwa ‘yan ɗariƙa ba su yarda da wannan almarar ba.

‘Yan Shi’a sun yarda da auren mutu’a kuma suna yin sa, su kuwa ‘yan ɗariƙa a wajensu wannan irin auren zina ce kawai.

---

[1] Domin ganin bambanci tsakanin yadda ‘yan Shi’a da Ahalus Sunna suke duban Imaman Shi’a, sai a nemi littafinmu **Ahalul Baiti a mahangar Ahalus Sunna da ‘Yan Shi’a**.

Amma duk da waɗan nan bambance-bambance masu yawa, ‘yan ɗariƙa, musamman ɗariƙar Kadiriyya, sun taimaka wajen yaɗuwar Shi’a a Nijeriya. Ya aka yi haka ta faru?

Ga alama, akwai dalilai guda biyu. Na farko: jahilcin yawancin ‘yan ɗariƙa dab a su san haƙiƙanin Shi’a bad a miyagun aƙidojinsu. Na biyu: munafuncin ‘yan Shi’a da yaudararsu, inda suka I amfani da taƙiyya, suka shige wa ‘yan ɗariƙa suna nuna cewa sun yarda a aƙidunsu da ayyukansu a lokacin da, a haƙiƙa, suna ɗaukar su a matsayin kafirai. ‘Yan Shi’a, waɗanda aƙidarsu ta taƙiyya ta ba su dama su yi kome ba kome,[1] sun shiga cikin ‘yan ɗariƙa suna yin Maulidi tare da su, suna sallah bayan su, suna halartar tarukansu na zikiri da wa’azi, da sauransu. Wannan sai ya yaudari ‘yan ɗariƙa, a yayin da suka ɗauka cewa ‘yan Shi’a ‘yan uwa ne abokan tafiya. Amma a haƙiƙa abin ba haka yake ba.

Su ‘yan Shi’a suna sane da cewa alaƙar su da ‘yan ɗariƙa alaƙa c eta yaudara, amma su Sufaye bayin Allah mutanen kirki bas u sani ba. Malaman Shi’a suna lasafta Sufaye ‘yan ɗariƙa a sahun nasibawa maƙiya Ahalul Baiti, kuma suna kafirta su baki ɗaya, kamar yadda suke kafirta sauran Ahalus Sunna tun daga kan Sahabbai, Allah ya ƙara musu yarda, har ya zuwa yau.

Babban shaihinsu mai suna Alhurrul Aamili, yana cewa: “Ka sani (ya kai mai karatu) cewa wannan suna, watau Sufanci, ya kasance ana amfani da shi ga wasu falasifawa ɓatattu ga barin hanya. Sa’an nan, daga baya, sai aka riƙa kiran wasu zindiƙai da shi, da wasu masu saɓa mana, maƙiyan Ahalul Baiti, irin su Hasanul Basari da Thauri da sauransu. Sa’an nan, wasu suka zo waɗanda suka bi tafarkinsu, irin su Gazali shugaban maƙiya Ahalul Baiti… Suka riƙa ganin cewa nasibawa da zindiƙai a kan gaskiya suke, sai suka bar lamarin Shari’a.”

---

[1] Domin ganin aqidar Taqiyya da yadda ta halasta wa ‘yan Shi’a su aikata abinda suke ganin haramun ne a wajen su, sai a duba littafinmu **Aqidar Taqiyya a wajen ‘Yan Shi’a.**

Ya ci gaba da cewa, "Shaihinmu mai girma, Shaihu Baha'uddin Muhammad Al'aamili, ya ruwaito a cikin littafin *Kishkul* cewa Annabi(SAW) ya ce, 'Alƙiyama ba za ta tashi ba sai wasu mutane daga al'ummata sun bayyana, sunansu Sufaye, ba sa daga gare ni. Kuma lallai su ne Yahudawan al'ummata, kuma sun fi kafirai ɓata, kuma su 'yan wuta ne.'"[1]

Za mu kula cewa a cikin wannan nassi, malamin ya kafirta manya-manyan shaihunnan Sufaye da malamansu, ciki har da Hujjatul Islam Algazali, wanda ya kira shi shugaban nasibawa, da Hasanul Basari wanda yawancin Sufaye suke ɗaukar sa a matsayin tushen tafarkinsu. To ina kuma ga sauran shaihunnai da waliyyai?

Haka nan, malamin Shi'awa ɗan hayaƙi, Ni'imatullahi Aljaza'iri, ya ƙulla babi musamman a cikin littafinsa, inda ya yi bayanin aƙidar malaman Shi'a ta kafirta dukkan 'yan ɗariƙa da shaihunnansu da waliyyansu saboda sun yarda da khalifancin Abubakar da Umar da Usmanu, kuma ya sifanta su da mafi munin siffofi.[2]

Wannan yana tabbatar da abinda muka faɗi cewa, kusanta 'yan ɗariƙa da 'yan Shi'a suke yi ba wani abu ba ne face yaudara, don su samu magoya baya daga almajiransu. Abin takaici shi ne har yau malaman ɗaiƙu da mabiyansu bas u gane ba. Sai yaushe za su farka?

## Yanayin Yaɗuwar Shi'a a Yau

[1] A duba **Risalatul Ithnai Ashariyya fil Raddi alal Sufiyya** na Alhurrul Aamili, shafi na 13-16.

[2] A duba **Al'anwarul Nu'umaniyya,** babin **Zulumatun fi Ahawalis Sufiyyati wal Nawasib,** bugun Madba'atu Baab, Tibriz-Iran, ba tarihi, mujalladi na 2 shafi na 305.

Tun zuwan Shi'a Nijeriya, ƙungiyar ta taka matakai uku na yaɗuwa kamar haka:

Na ɗaya, matakin yaɗuwa a lokacin *taƙiya* da munafinci da yaudara. Wannan shi ne lokacin da shugabannin Shi'a suka yi ta kira da sunan gwagwarmaya da sabunta addini da kafa hukuncin Musulunci. A wannan yayi, ƙungiyar ta yaɗu yaɗuwa mai yawa a lokaci ƙanƙani sakamakon ƙishirwar matasa ta sauyi da kuma rashin sanin haƙiƙanin abinda da'awar ta ƙunsa a wannan mataki.

Mataki na biyu, shi ne lokacin da Malam Zakzaki ya fito fili ya bayyana cewa lallai Shi'a yake yi bayan *taƙiya* ta tsawon shekara goma sha biyar ko sama da haka. A wannan lokaci ƙungiyar ta rabe biyu kusan a tsakiya, inda a shekarar 1995 aka samu ɓullar ƙungiyar *Jama'atu Tajdidil Islam* wacce ta yi shelar barrantarta daga tafarkin Rafilanci kuma ta yi wa shugabancin Zakzaki tutsu. Koƙarin matasa dake ɓangaren J.T.I. da ƙungiyar Izala da kuma malamai da almajirai masu bin tafarkin *Salafiy*a, ƙoƙarin waɗan nan gaba ɗaya wajen tona asirin Shi'a ya kawo tsaiko ga yaɗuwarta, musamman a birane inda a da a nan ne ta fi yawan mabiya.

Ga alama a yanzu, Shi'a tana shiga mataki na uku na yaɗuwa, inda masu aikin yaɗa ta suka mayar da hankali zuwa ƙauyuka da yankunan karkara. A cikin 'yan shekarun nan, biyu zuwa biyar, Rafilanci yana yaɗuwa kamar wutar daji a ƙauyuka saboda ƙarancin ilmi da wayewa ta addini da kuma cewa yawancin masu wa'azi suna tattara ƙarfinsu a birane, sai kaɗan ke fita dawa. Wannan ci gaba, ko kuma ci baya za mu ce, da aka samu yana da haɗarin gaske. Dalili shi ne, dama Shi'anci jahilci ne, kamar yadda mai karatu ya riga ya gani, to idan aka haɗa shi da jahilcin dake akwai a karkara, to an samu itace jiƙe jagab da kananzir, babu abinda ya rage sai ƙyastun wuta! Idan haka ta faru, Allah ya tsare, za mu wayi gari a wani yanayi wanda ɓarnar Maitatsine da ta'addancin Kiristoci za su zama tamkar wasan yara. Allah ya kiyashe mu fargar jaji.

## Rufewa

A cikin wannan taƙaitaccen littafi mun ga yadda Shi'a ta shigo Nijeriya kuma mun ga dalilai da suka taimaka wajen yaɗuwar ta. Kuma sharrin wanan mugunyar ƙungiya ga addini da rayuwar duniya a yau ba sai an faɗi ba; tun da abu ne wanda kowa yake iya gani da idanunsa.

Don haka ya zama wajibi ga dukkan Musulmi, ɗaiɗeku da ƙungiyoyi da hukumomi, su taimaka wajen yaƙar wannan ƙungiya, domin ceto waɗanda suka riga suka faɗa cikin ta da tsayar da yaɗuwar ta. Bai kamata wani ɓangare na al'umma ya yi kamar babu ruwansa ba a wannan harka; saboda yaɗuwar Shi'a matsala ce wacce ta shafi kowa da kowa.

Kuma dole ne waɗanda suka taimaka a baya wajen yaɗuwar wannan ƙungiya, su yi KAFFARA a yanzu ta hanyar taimakawa wajen yaƙar ta. Saboda haka, malaman ɗariƙu da almajiransu, da 'yan Boko waɗanda a da suka yi Buraza, da kuma 'yan ƙungiyar Jama'atu Tajdidil Islam, waɗanda suka tuba daga yin Shi'a amma suka koma gefe suka zama 'yan kallo, suna da nauyi na musamman wajen yaƙar wanan mugunyar ƙungiya da ganin bayan ta.

Kuma koda yake haɓakar ƙungiyar da yawan hayaniya da barazanar ta suna ba wasu mutane tsoro, amma mu da muka san ɗabi'arta muna iya tabbatar wa da mutane cewa yaƙar ta da kawar da ita daga doron ƙasar Nijeriya abu ne mai sauƙi, in Allah ya yarda. Shuru na mutane shi ke sa ta yaɗuwa ba wani abu ba. Don haka lokaci ya yi da kowa zai ba da tasa gudunmawa.

Allah ya yi mana taimako. Shi ne abin dogaron mu.